Ƙungiyar kasar japan mai kula
Da hulɗar Ƙasa da Ƙasa.

Ma'aikatar ministar
Aikin gona

Binciken dausayoyin yankin sahel a jamhuriyar Nijar



Littafin bada horo bisa ga kiwon kihi cikin korama

(Domin unhanin mahalatar horo)

Watan juli 2007

Ƙungiyar Ƙasar japon mai kula da albarkar tsanwa (J.Green)

Wallafawa da Ƙungiyar ADA cikin yarjejeniya tare da EDOS

# KANUN LITTAFI

Gabatarwa ..........................................................................3

I. Gurori da sakamakon littahi ..................................................4

II. Kalmomi dangance da keɓeɓɓen wuraren kamun kihi cikin dogon lokaci..........................................................................4

2.1. Fassarorin sauren kalmomi................................................4

2.2. Ma’anar keɓeɓɓen wurin kamun kihi cikin dogon lokaci..........4

III. Husa’ar kiwon kihi cikin ƙorama .............................................5

3.1. Husa’ar kiwon kihi ..........................................................5

3.2. Kulawa da wurin renon kihi...............................................5

3.3. Matakkan ɗauka don kare wurin .......................................5

IV. Husa’o’in renon kihi ..........................................................6

4.1. Ma’ana da ire-iren renon kihi.............................................6

4.2. Abobuwan da suka Ƙumshi renon kihi.................................7

4.3. Tahiyarda manya-manyan wuraren kamun kihi....................7

V. Husa’ar ajiya kihi .................................................................7

VI. Unhani da tattalin kayan kamun kihi ....................................10

6.1 Mahimmatan kayan kamun kihi ..............................................10

6.2. Manya-manyan matsaloli da ake fuskanta cikin tattalin kayakin kamun kihi ..........................................................................11

## Gabatarwa

An wallafa wannan littafi domin ba mahalartan horo cikakken horo bisa kiwon, ajiya kihi da tattalin kayan kamun kihi.
Mahalaratan taro sukan shugabancin waye ma mutane kai da basu horo bisa kiwon kihi.

- Ma kaman kihi su sunadda cewa ya kamata ayi tattalin kihi cikin tsawon lokaci.
- Su yi aiki da dokar da aka kafa domin kariya keɓeɓɓen wurin kiwon kihi a raba daidai-daidai arzikin da kiwon kihi ya kawowa jama'a.

Saboda haka, a Ƙarshen taro yakamata su iya maimaitawa mutanen gari sanin da suka samu wajen horo.
Wannan littafi na ɗauke da wasu dubaru ma su bada damar sani yadda ake kiwon kihi tare da cin unhanin husa'ar.

## I. Gurori da sakamkon littafi

Wannan littafi yakan ba mahalartan horo damar maimaita ma mutanen gari horon da suka samu bisa ga kiwon kihi.

Gurorin littafi sune :

- Ba mahalartan horo damar gane waɗannan kalmomi :
  - Kɛɓɛɓɓen wuraren kamun kihi cikin dogon lokaci
  - Husa'o'in kiwon kihi
  - Husa'o'in ajiyar kihi
  - Husa'o'in tattalin kayan aiki kihi
- Bada damar aiki da sanin da aka samo a wajen horo.

## II. Kalmomi dangance da kɛɓɛɓɓen wuraren kamun kihi cikin dogon lokaci.

### 2.1. fassarorin sauren kalmomi.

- Kamun kihi: duk ayyukan dake shiga cikin aikin kihi, wuraren da ake Ƙɛɓewa, ruwan da ake unhani da shi domin samu kihi.
- Ƙɛɓɛɓɓen wuraren kamun kihi: wurare ne na ruwa da ake gyarawa domin kiwon kihi da cin unhaninshi cikin dogon lokaci,
- Masayan kihi : mai shiga tsaƘanin ma su kamun kihi da ma'unhaninshi.
- Manyan gurubban ruwa ma su kihi : wurare ne da ake Ƙɛɓewa na kiwon kihi ana cin unhaninshi ta hanyar ka'idodi da aka kafa.

### 2.2. Ma'anar Ƙɛɓɛɓɓen wurin kamu kihi

Hus'a ce da aka ƘirƘiro domin kyautatawa ga duk ma su rayuwa su ta hanyar aikin kihi (masu kamu kihi, Masayan kihi, ma su saida kayan kamu kihi). A na aiki da ka'idodinta ta wannan hanyar :

- Sa hannun al'ummar gari wajen zaɓen irin ayyuka da kayan aiki kihi,
- Ɗaukar matakkai domin daidaita yawan kihi da za a kama da yawan wa inda ke cikin ruwa,
- yin ayyukan kariyar wuraren kamun kihi (Ƙururube)
- hana unhani wajen kamu kihi tare da wasu kayan aiki.
- Mutanen gari su san matakkan ragiya ɓacewar kihi (gasa kihi)
- Ɗaukar matakkan bada horo na aiki da ƙɛɓɛɓɓen wurare kiwon kihi, a rika tsarin su da waye ma jama'a kai

III. Husa'ar kiwon kihi cikin ƙorama

3.1. husa'ar kiwon kihi

ya kamata asan irin ƙoromar da za a kiwota kihi cikin domin samun damar sani irin kiyahun da suka dace.

- A san yawanci lokacin ruwan (mai jimawa ko marar jimawa ne). In ruwan masu jimawa ne, akan kiwota irin kihi mai babbar daraja ba tare da an damu ba da tsawon lokacin girmanshi. I dan ko ruwan marar jimawa ne ayi unhani da irin kihi mai zafin girma.
- Wajen kala ruwa : duk ire-iren kiyahu sukan iya rayuwa cikin ruwa mai kala tsanwa ko laka-laka. Amma in kala ruwan fari ne ko ja masu siffa burau ko ramboshi kaɗai kan iya rayuwa ciki.

Foto 1, 2 da 3 : wasu ire-iren kiyahu da ake kiwota cikin yankin sahel


Gargaza
(aifuwa sosai/kawowar riba)


Burau
(mai rayuwa cikin kasa ko laka )


rambosh
(mai cin kananan kiyahu don daidaita yawon kihi cikin ruwa)

- Zirfin ruwa yakan ba kiyahu damar rayuwa, akwai daga cikin irin kihi masu so da marar so ruwa mai zirfi.
- Akan aiki da girman ƙoramar wajen sani yawan kihi da yakamata a sa ciki.

3.2. kulawa da wurin renon kihi

babbar matsalar batta wajen kiwon kihi, amma wajen cin albarkar kiwon da ake yi. Saboda haka akan zamanar da ƙaramin kwamiti da zai kula da ƙoramar (hana kamu kihi  da wa ɟansu kayan aiki da aka hana).

3.3. Matakkan ɗauka don kare kabeɓɓen wurin.

Matsaloli da ƙorama ke iya huskanta.

In ƙoramar batada kariya takan iya huskanta matsalar :

- ƙasa da laka dake iya shiga ciki, sukan kawo raguwar kihi ko ɓacewarshi,
- salte dake zama ciki yakan ɓata ruwan da kawowa mutuwar kihi

Matakkan kariyar ƙorama

In ƙasa na handama ƙoramar, a tsaida yaɗuwar ƙasar dake a kewaye ta hanyar unhani da kara da rasshan itatuwa…
In wasu manya-manyan ruwa na gudanowa su shiga cikin ƙoramar, a gina ƙaramin gandari mai tace salte domin kada ƙasa da laka su mamaye ta.
Akan iya ginar rabin wata cikin kururuban don a kare ƙasar da lakar.
Rabin wata akan ginasu cikin ƙasa tare da tsawon cm 20 zuwa 30 da tsawon diyamita m3 zuwa 4.
A sa m3 zuwa 4 tsakanin rabin wata zuwa wani rabin wata. Su kasance a karkace da inda ruwan ƙoramar ke zuba.
In ana so a ƙarfafa aikin rabin wata wajen tsaida ƙasa a kewayen ƙoramar. A shipka itatuwa cikinsu, misali a tsakiya, gaban ramin, a kowane gehe na ramin.

Tattalin ayyukan kariyar ƙoramar

Akan kawo gyara da zarar an gani wata matsala dangance da ayyukan kariyar ƙoramar. Domin rayar da ita, akan tsare shipkar da ke ciki da yankin manya-manyan itatuwa.

Ma'anar tsarin kai da kai

Mutanen gari su tsara kansu da kansu don kariyar ƙorama sune:
Masu kamun kihi, mai aikin gandari don ban ruwa itatuwa da maikiwo don ban ruwan dabbobi. A takaice aikin kariyar ya shafi kowa da kowa.

Jama'a kan kafa dokokin kariya, na bada damar unhani da ƙoramar da kafa hanyoyin cin tara.

Wannan tsari da aka kafa wajen ƙorama zai zamnar da hulɗa tsakanin hukumomin galgajiya, na kwamin da ma'aikatocin gwamnati domin samu taimako. Biyan buƙatu na kyautata rayuwa jama'a a game da na kariyar ƙorama.

## IV. Husa'o'in renon kihi.

4.1 Ma'anar da ire-iren renon kihi.

Datattun wurare ne na kiwon kihi. Akan samu :

- Renon kihi da ake cikin manya-manyan wurare : Akan samu ƙaramcin kihi da ƙaramcin kashe-kashe kuɗi,

- Renon kihi cikin madaidaitun wurare : Akan samu kihi mai yawa, da kuɗi mai dama  ta hanyar taki da abincin da ake sama kihi cikin ruwa,
- Renon kihi cikin ƙananan wurare : Akan kiwon kihi mai yawa cikin akulki, garke, ƙanana gurubban ruwa... : kihin yakan rayuwa ta hanyar abincin da ake bashi.

Renon kihi cikin manya-manyan wurare ita ke zuwa da renon kihi cikin ƙorama. Ana gudanar da aikin ta haka :
- Daidaita yawan kihi wajen zaɓen iri, ya zamanto kiyahun na iya rayuwa tare, miyagun kada su hice kashi 10 bisa 100,
- A kama kihin da kayan aiki kamar : taru, birgi, shillin mamari
- Da hukewar ƙoramar domin kareta da matsaloli.

## 4.2. Abubuwan da suka ƙumshi renon kihi.

Abincin kihi na fitowa cikin ruwan da yake, in ana renon kihi cikin manya-manyan wurare. Kenan irin ruwan, wurin ko irin dabagar da yake ciki ke bashi damar samu abinci.

## 4.3. Tahiyar da kiwon kihi cikin manya-manyan wurare.

Hanyoyin su ne :

- Daidaita yawan kihi wajen zaɓen iri a tabbatar da cewa kiyahu na iya rayuwa tare, ya zamanto yawan miyagun kihi ba zai fice kashi 10 bisa 100
- Akan kamun kihi da kaya kamar : taru, birgi, shilli ... taru mai yasa (2 ko 3) da waɗansu mamari (duban foto lamba 12 zuwa 1) domin barin wayansu ƙanana  da za su rayu su yaɗa iri. Akan unhani   da wasu kayan aiki don a daidaita yawon kihi da yakamata a kama. Misalin gidon Bado ana unhani da taru wajen kamun burau, mamari wajen kamun ramboshi da birgi wajen kamu gargaza. Lokacin da aka samun kihi shine lokacin zahi. Kiyahu kan yawan neman abinci da neman aifuwa. Amma yakamata a cikin wannan lokaci a keɓe ƙaramin lokaci da za a tsaida kamun kihi domin barin kihin ya yawanta.
- Akan hoke ƙoramar domin kare wasu matsaloli.

## V.  Husa'a ta ajiyar kihi.

### Donmi ake ajiyar kihi?

Kihi yakan cikin cimaka mai zafi ɓacewa. Akan saida shi cikin ƙaramin lokaci in ba a so a bazarashi: saboda haka akwai husa'o'in adana kihi. Ajiya cikin wuri mai sanyi, shanyawa, gishirintawa, gasawa… husa'ar da tahi mahimmanci ga mazamnan ƙauye Ita ce gasawa. Akan samu

matsalar itatuwa da gasheshen kihi, ta wannan hanya. Da yake  ana huskantan matsalar itatuwa cikin ƙasashen yankin sahel unhani da murhun zamani na gasa kihi “ALTONA” kan iya biya buƙata.

## Ma’anar murhun zamani na gasa kihi « ALTONA »

« ALTONA » murhun zamani ne na gasa kihi. Yakan jima hiye da murhun galgajiya wajen tuya. Yakan bada gasasshen kihi ba da ɓata itatuwa ba.



Foto 4 : murhun zamani ALTONA

## Kayaki na ginin murhun ALTONA

I dan ana gini murhun ALTONA, a samu birgunan laka, taron waya, tol, kusoshi, itatuwa, ƙarahuna da maliƙin ƙohar murhun





Foto 5 da 6 : kayakin ginin murhun ALTONA

Inda yakamata a gina murhun ALTONA.

Mutun na gina shi wurin da ya ke iya wasu ayyukanshi tare da samun damar kulawa da aikin murhu.

Alamomin murhun ALTONA

Akan gina murhun da babbar sukurwa mai m1 da 80 da ƙaramar sukurwa mai m1da 60 da tsawon rami cm30 zuwa 40.

Ginar murhun ALTONA.

- Akan sa cikin rami jeri guda na birgi ;
- A gina katanga mai tsawon m1, ai unhani da cm45x45 wajen jera birguna farko ;
- A bar murhun ya bushe kwana 2 zuwa 3 bayan an gina shi ;
- Akan jejjera ƙarahuna bisa murhun;
- A yaɗa ragar waya bisa karahunan ;
- A bar raga wayar ta ɗan sabko daga ginar murhun kamar cm10;
- A ci gaba da gini bisa ragar waya hal m1 amma ayi unhani da cm 65x65 bayan an aza jerin farko na birguna, daga bayan murhu ayi gina mai tsawon cm85,
- Ayi huda biyu ga ɓangaren biyun na ɗakin gasa kihin;
- Ayi tudu bayan an ƙare gini ɗakin gasa kihi;
- A bar ɗakin gasa kihin ya bushe kwana2 zuwa 3;
- A aza mafyaɗai na itatuwa masu ƙwari bisa katangar kafi a aza tol ;
- Tol in ya sabko gina da m10 ta wajen tudu, a kange shi da kyau ga mafyaɗai;
- Akan iya ruhe murhun da itatuwa tare da laka;
- A kafa gambu a ɗakin gasa kihi kafin a sahe murhun (gamin laka da hakki);
- A fidda kayan cikin kihi, a wanceshi a rabashi gida biyu in babban kihi ne, a shanya kihin (bisa tabarma, ragar waya, zana ….) don fidda rowan dake ciki;

- Bayan kihin ya bushe akan jerashi bisa ragar waya ta ɗakin gasa kihi;
- A bar wurare emtinsu bisa ragar,
- A bar wurare emtinsu ga duk gehe huɗu da tsaƙiyar raga don iska ya ratsa ko ina, ya gasa kihin ;
- Bayan an sa duk kiyahun cikin murhu, ayi unhani da itatuwa masu ɗan kabri masu jima suna ci;
- Bayan an sa kihin da za a gasa, a kunna wuta, a ruhe gambun ɗakin gasa kihi da hudodin san iskan murhu;
- Gasawar na jima awa biyu zuwa ukku.

## VI. Unhani da tattalin kayan kamun kihi

### 6.1. Mahimmantan kayan kamu kihi





Foto 7 da 8 : kayakin kamun kihi taru , birgi , mamari....



Jirgin ruwa na kwatako

### 6.2. Manya-manyan matsaloli da ake huskanta cikin tattalin kayakin kamun kihi tare da mattakan ɗauka

Tattali ya shafi duk kayakin kamun kihi su taru ka jirgin ruwa. Akan ruhe duk wata huda da zarar an ganeta ga jirgi.

Akan shafa mishi man kaɗe ko wace shekara domin kare mutawar kwatakinnai. Su kuma tarun da an fiddosu daga ruwa a shanyasu a innuwa. Inda ya ɓace a gyara.